Mafi alherinku zamanina, sannan waɗanda suke biye musu, sannan waɗanda suke biye musu

Daga Imran ɗan Hussain - Allah - Ya yarda da su - ya ce: Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: «Mafi alherinku zamanina, sannan waɗanda suke biye musu, sannan waɗanda suke biye musu» Imran ya ce: Ban sani ba shin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agatre shi - bayan nan ya ambaci ƙarni biyu ne ko uku, Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: «Lallai a bayanku za'a samu wasu mutane zasu dinga ha'iinci ba'a amince musu ba, sunayin shaida ba tare da an nemi shaidarsu ba, suna bakance ba sa cikawa, kuma ƙiba zata bayyana a cikinsu».

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa mafi alherin ɗabaƙa ta mutane masu taruwa a zamani ɗaya sune ɗabaƙar sahabban da a cikinsa akwai Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - da sahabbansa, sannan waɗanda suke biye musu cikin muminan da suka riski sahabbai amma ba su riski Manzon Allah ba, sannan waɗanda suke biye musu sune masu biyewa tabi'ai, sahabin ya yi kaikawo a cikin ambatan waɗanda suke biye musu ga ƙarni na huɗu. Sannan tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: Lallai a bayansu za'a samu wasu mutane zasu dinga ha'inci, mutane ba za su amince da su ba, kuma zasu dinga yin shaida kafin a nemi shaida daga garesu, zasu yi bakance ba sa cikawa, zasu dinga yalwatawa a ciye-ciye da abubuwan sha har sai ƙiba ta bayyana a cikinsu.

النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee